Kada ɗayanku ya ce: Ya Allah Ka gafarta mini in Ka so, Ka yi mini rahama in Ka so, Ka azirtani in Ka so, ya ƙudirce niyyar rokonsa, lallai Shi Yana aikata abinda Yake so, babu mai tilasta Shi

Daga Abu Huraira - Allah Ya yarda da shi - daga Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya ce: "Kada ɗayanku ya ce: Ya Allah Ka gafarta mini in Ka so, Ka yi mini rahama in Ka so, Ka azirtani in Ka so, ya ƙudirce niyyar rokonsa, lallai Shi Yana aikata abinda Yake so, babu mai tilasta Shi". Kuma riwayar Muslim: "Sai dai ya ƙudirce niyyar tambaya kuma ya girmama kwaɗayi, domin Allah wani abu da Ya bada shi ba ya yi maSa girma".

[Ingantacce ne] [Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi]

Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya yi hani daga rataya addu'a da wani abu koda ya kasance da Mashi'ar Allah ne (ganin damar Allah) domin hakan wani al'amari ne abin sani abin sakankancewa cewa shi ba'a gafartawa sai idan tsarki ya tabbatar maSa Ya so, kuma babu wata ma'ana ga sharɗanta Mashi'a; domin cewa ita kaɗai ana sharɗantata ne ga wanda ya inganta daga gare shi ya yi aiki ba tare da ya so ba da tilastawa da waninsa daga abinda Allah - tsarki ya tabbatar maSa - Ya tsarkaka daga gare shi, haƙiƙa tsira da amincin Allah su tabbata agare shi ya bayyana a cikin ƙarshen hadisin da faɗinSa lallai shi Allah babu mai tilasta shi, kamar yadda cewa Allah babu wani abu daya da ya bada shi yake girmama a gareShi, kuma Shi ba mai gajiyawa bane kuma wani abu ba ya girmama a gareShi har ace: Idan Ka so, kuma rataya shi da Mashi'a wani nau'i ne na wadatuwa daga gafararSa, to faɗin mai faɗa: Idan Ka so Ka bani kaza to Ka aikata, ba'ayin amfani da wannan sai tare da wanda ya wadata daga gare shi, ko tare da wanda ya gajiya, amma tare da mai iko kuma tare da mai buƙatuwa gare shi to cewa shi ya ƙudirce niyyar roƙonsa, kuma ya yi roƙo irin roƙon mabuƙaci mai tsananin buƙatuwa zuwa ga abinda ya roƙe shi, kuma ya fake zuwa ga Allah; domin cewa Shi Mawadaci ne cikakke, Mai iko a kan dukkan komai.

http://sunnah.global/hadeeth/ha/show/5978